# Ka kasance a duniya kamar kai baƙo ne ko mai ƙetare hanya

Daga Abdullahi ɗan Umar - Allah Ya yarda da su - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Ka kasance a duniya kamar kai baƙo ne ko mai ƙetare hanya", Ibnu Umar ya kasance yana cewa: Idan ka kai maraice to kada ka saurari safiya, idan ka wayi gari to kada ka saurari yammaci, ka yi riƙo daga lafiyarka dan rasshin lafiyarka, kuma daga rayuwarka dan mutuwarka.
[Ingantacce ne] [Buhari ne ya rawaito shi]

Ibnu Umar - Allah Ya yarda da shi - ya ambata cewa Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya riƙe kafaɗarsa - ita ce mahaɗar damuttsa da allan kafaɗa - kuma ya ce masa: Ka kasance a duniya kamar kai baƙo ne, wanda ya zo garin da ba shi da masauki a cikinsa da zai sauka, kuma babu wani mazaunin da zai kwantar masa da rai, ya kaɗaita daga iyalai da 'yan uwa, waɗanda sune sababin shagalta daga Mahalicci, kai ka kasance mafi tsanani daga baƙo shi ne mai ƙetare hanya mai neman ƙasarsa; domin cewa baƙo zai iya zama a garuruwan baƙunta kuma ya zauna a cikinsu, saɓanin mai ketare hanya mai nufin gari, domin cewa daga sha'aninsa saukakawa da rashin tsayuwa, da kwadayi akan saduwa da garinsa, kamar yadda matafiyi ba ya bukatuwa ga sama da abinda zai kai shi zuwa karshen tafiyarsa, haka nan mumini ba ya bukatuwa a duniya sama da abinda zai kai shi wuri. Sai Ibnu Umar ya yi aiki da wannan nasihar kuma ya kasance yana cewa: Idan ka wayi gari to kada ka jira maraice, idan ka shiga maraice to kada ka jira safiya, ka ƙirga kanka a cikin ma'abota ƙaburbura, kuma cewa rayuwa ba ta kaɗaita daga lafiya da rashin lafiya. Ka yi gaggawa a lokutan lafiyarka da aikin ɗa'a dan rashin lafiyarka; ka ribaci ayyuka na gari a cikin lafiya kafin rashin lafiya ta tsare tsakaninka da su, ka ribaci rayuwarka a duniya, ka tara abinda zai anfaneka bayan mutuwarka.

https://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/4704